

An Karɓe Mu!

Yesu ya ɗauki ƙiyayyarmu domin mu sami amincewar Sa a wurin Uba



Furta Kalmar Allah
Daga Derek Prince

Kiyayya, a taƙaice, tana nufin yanayin da ba a buƙatar ka ko kuma jin cewa, ko da yake kana son mutane su ƙaunace ka, babu wanda ya yi hakan. Ko kuma zai kasance kana son kasancewa a cikin wata ƙungiyar mutane wadda kake jin an ware ka daga ciki - kamar dai a koyaushe kana leƙe daga waje. Ɗaya daga cikin dalilan da ya sa mutane da yawa a yau suke fuskantar ƙiyayya shi ne yanayin al'ummar mu da kuma matsi, musamman ma waɗanda ke kawo rabuwar iyali.

Mecece kishiyar ƙiyayya? Amincewa ce. Ina son sashin ƙarshe na Afisawa 1:6; wanda ke cewa:

> "Wanda [wato, Allah] ya ba mu kyauta hannu sake saboda Kaunataccensa."

Yesu, tilon Ɗan Allah na haƙiƙa kuma makaɗaicin Ɗansa, wanda aka ƙi shi domin mu, mu ‘yan tawaye marasa amfani, domin mu sami amincewarsa a wurin Uba. Tabbaciyar mafita ga matsalolinmu ita ce mu gaskata cewa Yesu ya ɗauki ƙiyayyarmu domin mu sami amincewar Sa a wurin Uba.

Iyalin Allah shi ne iyali mafi kyau. Babu wanda ya ke daidai da shi. Ko da iyalin ka ma ba su kula da kai ba—wataƙila mahaifin ka ya ƙi ka ko mahaifiyar ka ba ta da lokaci domin ka—duk da haka Allah yana son ka. An karɓe ka. Kai abin kulawarsa ne da ƙaunar sa ta musamman. Duk abin da Ya ke yi a duniya domin ka ne.

Idan Allah ya ce an karɓe mu, ba yana nufin cewa an yarda da mu ba ne kawai. A koyaushe yana da lokaci domin mu. Abu ɗaya kawai da ke ɓata masa rai shi ne idan muka guje shi na tsawan lokaci. Ba ya kawar da mu ya sa mu a lungu ya ce, "Ka jira. Ina da uziri. Ba ni da lokaci domin ka." Maimakon haka, yana cewa, "Na damu da kai. Ina son ka. Barka da zuwa. Shigo. Na daɗe ina jiran ka."

Na gode maka, Yesu, saboda aikinka a kan gicciye. Ina furta cewa "Allah ya karɓe ni cikin Kaunataccensa," kuma ya marabce ni. Yesu ya ɗauki ƙiyayya ta domin in sami amincewar Sa a wurin Uba. Amin.


© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.

Abincin Yini ★

Kwafi: WD-B097-141-HAU

Sabuntawa ta ƙarshe: 24 Sept 2026

Yanar Gizo: Derekprince.com/ha/resources



© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.